[3:36pm, 2/9/2016] presido: Auran gata_01_ kwance take tayi rigingine akan kujera ta tsira ma TV ido tana kallon cartoon a MBC 3 hankalinta gabaki daya ya karkata a kallon da takeyi ko kadan ka kalleta zakasan batada damuwa bata wuci shekara goma sha biyu ba kallonta takeyi hankali kwance batare data san wainda ma suke shiga da fita acikin parlon ba duka kawai taji an daka mata a baya tajuya dasauri suka hada ido dawanda yaduketa din takwalla kara tamike tabishi dagudu yana daria shima yaruga aguje tana ihu tana ya yazeed wallahi ka tsaya in rama wallahi ni sai narama juyowa yayi yamata gwalo yakuma rugawa dagudu sukaci karo da mami tana saukowa daga sama dasauri yayi bayanta yaboye yana daria mami tace kaji mun da ku kenan bakwai gajia da shegen fadan Nan naku na tsiya daria yayi yasaketa yayi sama dagudu saida yaje kusa da dakin shi yace yazeenat taruga dagudu tayi hanyan dakin nashi tana ihu tace wallahi mami ki gaya mai ya tsaya in rama mami tace tsakanin kune keda wannan dan'uwan naki kukan shagwaba tafashe dashi takarasa saman tana wallahi ya yazeed ka tsaya in rama Allah ni saina rama gwalo yamata yace i'm d Winer takuma rugawa dagudu tace yhu can't escape frm me saida takusa dakin yakuma mata gwalo yarufo kofan gwaram yakulle tazube ajikin kofan tana bubbugawa tace wallahi saina gaya ka da daddy wallahi ni bazan yadda ba yhu better open d door ma tunkun in hadaka da daddy yazeed dasauri yabude kofan tayi kanshi dagudu tafada jikinshi tana dukanshi tako ina yanata daria saida tagaji takyaleshi tana nishi kaman wacce tayi seran gudu tayi tsalle tace yee narama nandanan kuma tafara yarfe hannu tana tabe baki yazeed yakamo ta yazaunar da ita akusa dashi yace i'm so sowie my little princess sister yakama kunnan shi yana yarfe hannu shima daria takwashe dashi tamai gwalo tamike dagudu tabar dakin tana daria shima dariyar yayi yabita yana kiranta yazeenat [4:53pm, 2/9/2016] presido: 0_02_ dagudu tafada jikin mami tana daria mami tace kudai kam baku gajia da yan tsalle tsalle dagake har yayan naki kuma kinzo kin dane mun jiki yazeed yarugo dagudu yasamu waje yazauna yana nishi mami takalleshi tace kaidai ka girma Amma haryau bakasan ka girma ba shekara goma 18 ai kamata yayi ka nutsu kullim Jinka kakeyi kaman wani karamin yaro andai kusa tafia skull a kyaleni in huta a shagwaba ya matso inda take yace kai mami nifa haryau yarone dasauri yazeenat takalleshi tayi daria tace mami wai kinji har yau shi yarone ki kalli har yafara yin gashin fuska mami tafashe da daria yazeed yace mami kin ganiko kina son ta raina ni mami tace aini bazan shiga tsakanin kuba dan duk wanda yashiga tsakaninku yaji kunya yazeed yadan kwanta a kafadan mami yace nidai mami bana son rabuwa da sister pls mami kice ma daddy nafasa zuwa Istanbul din pls yazeenat tadauka tace pls mami kinga banason rabuwa da yayana pls kicema daddy yabarshi anan mami tamike tace niku dagani rigimammu kawai saiku bari idan daddyn naku yadawo saiku tareshi ku fada mai yazeed ya rafka uban tagumi yazeenat ta isa inda yake tace ya yazeed fushi kake da mami ko nima nayi fushi da ita tunda tasaka kayi fushi janyota yayi! Yayi murmushi yace kin manta anche babu kyau fushi da iyaye dasauri tazaro idanuwa tace shikenan zan shiga wuta yazeed ya kwashe da daria tazira mai idanuwa ta bangaje shi tamike dasauri tana turo mai baki tace kuma minyi fada kuma zance ma daddy yatafi dakai cen Istanbul tayi waje dagudu jikin shine yaji yayi wani sanyi duk sanda aka ambaci tafiyanshi Istanbul sai yaringa jin wani iri bazay iya tafia yabar yazeenat ba yana matukar son kanwar shi baida kamanta dakyar yamike yayi waje cen yahango ta tana wasa dakarfi yace buddy tajuyo ta murguda mai baki taci gaba da abunda takeyi karasawa inda take yayi yazukunna a gabanta yakama kunnan shi ya lagwabar dakanshi yace i'm so sowie my lil sis juyowa tayi takalleshi takuma murguda mai baki tace daga yau bakai

bane yayana ya tahir ne yayana nandanan yanayin shi yachanza yamike yawuce yabata waje shi yarasa dalili duk lokacin data zabi tahir akanshi haushi yakeji to ai shine yayanta najini batada wani yaya daya wuce shi
[6:00pm, 2/9/2016] presido: 0_03_ da tunani kala kala yashiga parlo yawuce dakinshi kai tsaye wajajan magrib anfito daga masallachi daddy yashugo gidan dagudu yazeenat ta dane jikinshi tana daria shafa mata kai yayi yace my cwt daughter a hankali takai mai kiss a kumatu saida yakaita har tsakiyan parlo yadireta takalli yazeed tamai gwalo tace daddy yafi sona ko kallonta bayyi ba sannu dazuwa yama daddyn nasu mami ta anshi jakar dake hannunshi takai daki ta dawo tasamesu harsun fara kiciniyar zuba abinci murmushi tayi tace yaudau da alama yan uban ci zaa mun daddy yayi murmushi yace da yunwa yau nadawo kuma kinsan bana cin abinci a waje kujera taja tazauna itama tasa abincin nata sannan takalli yazeed da yazeenat tace yau kuma waya hadaku yazeenat ta turo baki tace wai dan nace yanzu shiba yaya na bane ya tahir ne yayana yazeed yagalla mata wani uban harara daddy da mami sukayi daria sukace babu me shiga tsakaninku zama ku shirya kanku ne dasauri yazeenat ta make wuya tace nidai nayi fada dashi kara hada rai yazeed yayi uban yan zuciya kenan inji daddy to fada dai yakusa karewa dan jibi zaka tafi nandanan idon yazeed ya chanza launi yazeenat ma sai tafara hawaye ta tashi ta matso inda daddy yake tarike mai hannu tace pls daddy a fasa tafiyan nan pls dad daddy yakalli mami ya girgiza kai yakama hannun yazeenat yace daughter bakiso yayanki yaje yayi ilimi yazama kaman sunusi lamido ina ce kince sunusi lamido na birge sbd ya iya speech daga kai tayi tana share hawayen fuskan ta tace eh daddy yace yauwa daughter kinga kenan zakiso yayanki shima yazama kaman sunusi lamido ko yazeed ne yatashi dasauri yana hawaye yabar wajan dasauri yazeenat tafashe dakuka tace kingani mami ko daddy yasa yayana kuka kuma kema dazu kinsa shi yayi fushi ni baruwana daku taruga dagudu tayi hanyan dakin yazeed daddy ya girgiza kai mami tace shakuwar yaran nan tayi yawa alhaji idan yazeed yatafi zamusha fama da yazeenat wajan rigima daddy yadan kurbi juice yace komin shakuwan su dole su rabu sabida komin daran dadaiwa yazeenat aure zatayi tabar yazeed mami tace hakane dakin yazeed tashiga tafada jikinshi suka fashe dakuka a tare a hankali yazeenat ta dago tashiga share mai hawayen fuskan shi tace yayana kadaina kuka daddy neko ba ruwan mu dashi yazeed yayi murmushi yakara kankameta yana fitar da kwalla yace yanzu nine yayanki ba tahir bako dasauri tadago tana shashshekan kuka tace kaine yayana kaine gabaki dayansu sukayi daria yakuma rumgume ta duk duniya baida abun so kamam kanwar shi yazeenat yana matukar kaunarta sabida ita kadaice kanwar shi su su biyu su mami suka Haifa shiyasa yanajin zafi idan aka ambaci tafiyan shi Istanbul dinnan baya son rabuwa da kanwar tashi a haka bacci yakwashe su yana rumgume da ita
[6:24pm, 2/9/2016] presido: 0_04_ suna gama cin abinci su mami suka shige daki jin shurun yayi yawa yasa takira me aiki tace taje tadauko yazeenat a dakin yazeed takaita dakinta ta kwantar da ita koda atuwa me aiki tashiga ta taddasu suna bacci dakyar tasamu ta babbare yazeenat daga jikin yazeed takaita daki mami tashiga tamata addu'a taja kofan tarufe sannan taje dakin yazeed ma tamai dan tasan bayyi ba sannan takoma daki tasamu daddy zaune akan gado da alama tunani yakeyi itama tasamu waje tazauna tace alhaji lafia daiko dasauri yadago yakalleta yace lafia lau ina tunanin irin shakuwar da yaran nan sukayi ne abun yana bani tsoro fa hajia bana son in karya alkawarin dana daukar ma dan'uwana mami tadan dafashi tace nikaina shakuwar tasu tayi yawa bansan yanda zanyi da yazeenat ba idan yazeed yatafi

karatun nan dan da alama bakaramin so suke yima junan suba alhaji yace bazan iya karya alkawarin dana daukar ma dan'uwana ba bazan taba gaya ma dayansu cewan bani na haifi daya daga cikin suba balantana yazeenat da har yau bata mallaki hankalin kanta ba nayi imani idan yazeed yatafi zata manta dashi shidin daine bazay manta dashi tunda da wayon shi kuma baba yariga yabama tahir yazeenat mami tace nikam Alh wannam auran zumuncin wallahi kwatakwata bana sonshi wallahi dan dai yazama dole ne alhaji yace ya zamiyi to fadan baban safana ne dole mubi umarnin shi ko minki ko munso da tunani barkatai suka kwana kada ache mami wacce take hango rabuwar yazeenat da yazeed bakaramin abu bane zaayi fama
[10:08pm, 2/9/2016] presido: 0_05_ washe gari tunda safe mami tasa su yazeed da yazeenat suka shirya dan a yau zasu safana yazeed zaije musu sallama fuskan nan ta yazeed a hade da alama he is not in d Moody doguwar riga aka sama yazeenat me kananan flowers ajiki red red tayi kyau sosai dan saida yazeed yadauke su pictures masu yawa tare tara daidai suka gama shiryawa sukayi breakfast mami ta rakasu har wajan mota takuma Jan kunnansu akan yawan fadan da sukeyi baya suka shiga driver yajasu suka tafi tunda suka shiga mota yazeenat take tafaman zubama yazeed surutu wanda shi ko kadan ma hankalinshi baya wajanta tafiyan dazayyi gobe kawai yake tunani tun daga farkon shiga garin suka faracin karo da yan uwa wani babban gida driver yayi parking suka bude motan suka fito yazeed yarike hannun yazeenat gagam suka shiga cikin gidan tun a tsakar gida suka faracin karo da mutane nanfa aka ringa ga yayyan yakubu kai tsaye dakin kakan su suka nufa wanda ake kira da baban safana suka zukunna har kasa suka gaida Shi saida suka zaga kauyen suka gaida yan'uwa yazeed yamusu sallama wajajan biyar na yamma suka jiyo suka dawo kaduna sune a hanya har magrib kwanciya yazeenat tayi akan cinyan yazeed tafara bacci kafa mata idanuwa yayi ji yakeyi kaman yadauketa yatafi da ita Istanbul gobe wajajan tara suka isa gida suna parking yadauketa cak yanufa cikin gida da ita kai tsaye dakinta yakaita yakwantar da ita yawuce dakinshi shima yakwanta ya lumshe idonshi sai ji yayi hawaye yawanke mai fuska shekara 8 ba wasa bane gaskiya zayyi missing gida sosai a haka bacci yakwashe shi daman gashi bakwai da rabi na safe jirgin su zay tashi washe gari tun asuba da suka dawo masallaci daddy yasa yazeed yashiga wanka yakuma ce yashirya kafin 6 daman masu aiki sun rigada sungama shirya mai kayan dazay tafi ko kadan basuyi yunkuri tashin yazeenat daga bacci ba saida yagama shiryawa tsaf mami tahado mai breakfast ta tasa shi agaba saida yacinye komi tass daddy yasa aka fitar kayan dazay tafi dasu akasa a mota daddy yarike mai hannu yace son muje hawayene yagangaro mai a fuska a hankali yace daddy bazanga lil buddy naba kafin intafi yakalli mami da itama kukan takeyi yace pls mami ki taso mum sister na muyi sallama daddy bai ankara ba yazeed yaruga dagudu yayi hanyan dakin yazeenat tana bacci yakarasa inda take a hankali yace bye lil sis am gana miss yhu dasauri yabar dakin yana share hawayen fuskanshi batare daya kalli su mamin shiba yayi hanyan waje mami da daddy sukabi bayanshi dasauri mami ta rumgume shi tana hawaye tace i'm going too miss yhu son ka kula dakanka kaji tsake shi tayi takoma cikin gida dasauri dan kukan dayaci karfinta daddy idonshi sunyi jajir yakama hannun yazeed yasashi amota sannam shima yashiga driver yajasu sukabar haraban cikin gidan yazeed fadawa jikin daddynshi yayi yafashe dakuka har suka kai airport bai daina kuka ba dakyar daddy ya lallashe shi 7:30 jrigin su yatashi daddy yashiga mota driver yaja suka tafi cike da kewar yazeed
[10:32pm, 2/9/2016] presido: 0_06_ sai wajajan karfe takwas ta tashi tashiga bayi tayi brush tayi

sallah sannan tafito daga dakinta tana murmushi bata tadda kowa a parlo ba dan haka kai tsaye tawuce dagudun ta tayi hanyan dakin yazeed dakarfinta tace ya yazeed tana shiga dakin taga wayam nandan idonta yakawo kwalla tabude toilet ma taga wayam nandanan tarude tafito daga dakin dagudu tana kuka da karfinta tace ya yazeed ina kake babu inda bata duba ba amma bata ganshi ba dagudu tayi dakin mami tana kuka tasamu mami akan gado baccima ta tashi cikin kuka tace mami ina ya yazeed sai tafashe dakuka dasauri mami ta diro daga kan gadon ta rumgume yazeenat tana lallashinta fizge jikinta tayi tana kuka tace mami ina ya yazeed dina ina shike mami da kwalla yacika mata ido tace yatafi wani ihu yazeenat tafasa tace mami kika barshi yatafi baimun sallama ba wayyo ya yazeed kadawo mami ce ta isa inda take dasauri ta rumgume ta tace ya isa haka ya isa a hankali bakinta narawa tace meyasa mami ya yazeed baimum sallama ba yatafi meyasa tana shashshekan kuka a hankali mami ta tsaketa tafara share Mata hawayen fuskanta tace ya isa haka ai zaku dinga waya dasauri yazeenat ta girgiza kai tana kuka tace ya yazeed yadaina sona mami shiyasa yatafi baimun sallama ba nima nadaina sonshi nadaina ssonshi mami dasauri tarufe mata baki tana girgiza mata kai tace yayan kine yana sonki sosai rumgume maminta tayi takuma fashewa dakuka wunin ranan dai komi bataci ba abu daya yatsaya mata a rai datake ta nanatawa ya yazeed bai mata sallama ba ranan wuni tayi kuka saida daddy da mami sukayi da gaske sannan suka sata taci abinci shima dan kadan taci yazeed yana sauka a Istanbul waya yafara kira number daddy yakira abunda yafara tabbaya daddy ina yazeenat daddy yayi murmushi yace tanacen tana ta kuka nandanan yazeed shima yaji hawaye yabata mai fuska tuni yakatse wayan yafada gado yana kukan rabuwa da tilon kanwar Shi

[7:29am, 2/10/2016] presido: 0_06_ shekaru na tafia lokaci naja mami ce daga daki take kwalama yazeenat kira dasaurinta tafito tsanye take da riga da skirt dinki bakaramin kyau yamata ba hannunta dauke da jaka kalar kayan sai wani hell shoe data saka me bala'in kyau dasauri tafito tace mami ganinan shiryawa fa nakeyi mami tace kedai wannan sakarcin naki dayawa yake jiyan nan kika gama cemun yau dawuri zaku shiga lectures amma kinje kina kwalliya kinfi hour kina abu daya yazeenat tazagaya tabaya ta rumgomo maminta tace to mami bagashi nashirya ba yauko breakfast bazan tsaya yiba mami tace aiko baki isaba sai kinyi breakfast zakibar gidan nan dawowa tayi kan kujera tazauna takama hannun mami tace pls kibarni intafi idan fa naje skull zanci snacks mami tace to sannu me bakin cin snacks murmushi yazeenat tayi tamike dasauri ta dauki jakarta taruga dagudu tana ma mami bye bye mami tace yazeenat da shirme tana fita tama motar ta key tashiga tabar haraban gidan kai tsaye hanyan makarantan su tanufa ta sanya wakan Akon tana bin wakan a hankali tana karkada kai cikin haraban makarantan tayi parking tafito kai tsaye inda kawayenta suke tanufa tasamu gu tazauna tace wai kuna nufin har yanzu baa shiga lectures ba fadila dake kusa da ita ta tabe baki tace inafa kinsan shegen mutumin nan tun 7 muke jiranshi amma shuru yazeenat tayi daria tace ai shiyasa na tsaya na kintsa a natse sbd nasan halin sa fadila tamike tsaye tace ku nayi gaba gashi cen zuwa nandanan suka mike sukabi bayanta suka shiga department dinsu sai wajan 2 suka fito ko tsayawa hirar da sukeyi yau yazeenat batayi ba tashiga motar ta tawuce wayar tace tayi ruri takai zara zaran hannunta tadauka murmushi ya bayyana a fuskanta takafa wayar a kunnan ta tace ya tahir dagacen yace gani a gida ke kawai nake jira wani ihu tayi tace i'm on my way yanzun nan pls ya tahir kada katafi ganinan takatse wayan takara ma motarta gudu uku daidai ta isa gida tana parking tafito dasauri har tanacin tuntube tashiga parlon mutane biyu

tagani sun juya mata baya bata iya tantance suwaye tana shiga tace ya tahir gabaki dayansu suka juyo a tare wani ihu tasaka tace ya yazeed dagudu taje tafada jikinshi sai kuma tayi saurin tsakin shi tahade rai mami da daddy dake saukowa daga sama sukayi daria yazeenat ta isa inda suke tace banyi murna da dawowan yaya ba sabida babu wanda yagaya mun zay dawo tayi dakinta dagudu yazeed a hankali yace yazeenat sarkin rigima mami tace aiga irin tanan saida nace afada mata amma alhaji kace aa wai za'ayi surprised dinta yazeed dasaurin shi yayi dakinta yasameta akan kujera tahade rai tana ganinshi tajuya mai baya yazeed yace am so sorry lil sis wlhi daddy ne yace ayi surprised dinki tahir yashugo dakin yana daria tamike tsaye kaman zata fita sai kuma tadawo tana murmushi tace yaya ka canza rike Mata hannu yayi yace muje parlo tahir yabi bayansu suka sauka kasa suka samu kujera suka zauna yazeenat tace mami yaya yakara girma yazama katoto daga mami har daddy saida sukayi daria daddy yace ke baice miki kin girma ba sai kece zaki cemai yagirma kada ki manta shekara 8 yabaki yazeenat ta turo baki tace yanzu ai i'm a biggal ko yaya yazeed yace haka abun yake yanzu sister tazama biggal daria gabaki dayansu sukayi sannan mami tace yaudai amma tahir yan ubanci kota kanshi bakiyi ba saita yayanki nandanan tazaro idanuwa sai yanzu ma ta tuna dashi wajanshi tanufa takama kunnan ta kaman zatayi kuka tace am sorry bro tahir yajuya yace bazanyi hakurin ba yazeed ji yakeyi kaman yatashi yashake shi haka kawai yaji yanajin haushin maganarma da sukeyi da tahir yazeenat tamake kafada tajuya tace daddy kagani ko yaki hakura ko daddyn yace tsakanin kune mami tace saiku tashi muje muck abinci yau beat food dinma akayi son yazeed yake kawait yayi yamike yayi gaba tahir yakamo hannum yazeenat yace naji nahakura my buddy a tare suka jera suka isa dinning yazeed nalura dasu
[8:56am, 2/10/2016] presido: 0_07_ daddy ne yace son Istanbul ya karbeka sosai bakaga yanda ya kara kyauba kodai achan za'a samo mana matane cokalin dake hannun yazeenat yafadi takai dubanta gun yazeed tana girgiza mai kai murmushi yayi yace kai daddy inani ina auran matan Istanbul aini matana daddy tana safana mami tace safana kuma wacece a safana kuma tahir yakai juice bakinshi yace ai mami inaga yar gida za'ayi dan yanzu sadiya ce kadai wacce batayi aure ba a safana nandanan fuskan yazeenat yachanza daddy yace gaskiya kayi tunani me kyau son yazeed yake kawai yayi yazeenat tamike tsaye tabar wajan Zuciyanta cike dajin haushin yayan nata dakinta tawuce to meke shirin faruwa dasune ita kam kishin yayan nata takeyi to meyasa kada dai acha son yayanta takeyi tashiga uku dan bata taba ganin yanda akayi soyayyan wa da kanuwa ba tahir shima yamike yabita dakinta yazeed yakai duban shi ga tahir a hankali yaja tsaki mami da daddy suna lura dashi abunda suke gudu zay faru
[9:31am, 2/10/2016] presido: 0_08_ abunda suke gudu shizay faru zaune tahir ya tadda ta tazuba uban tagumi yasamu waje yazauna yace buddy tayi saurin dagowa tadube Shi sai taji yana bata haushi murmushi ta kakalo tace ya tahir murmushi yayi yakama hannunta yamikar da ita tace yaya ina zakuma muje a hankali yace rakani zakiyi dan gida zantafi lagwabar dakai tayi tace kai ya tahir tun yanzu bazaka bari sai bayan magrib katafi ba girgiza kai yayi yace akwai abunda yakamata inyi tabe baki tayi tace to muje rike da hannunta suka fito parlo tahir yace mami da nina wuce gida daddy yace inace anan ma zaka kwana girgiza kai yayi yace aa daddy mami tace toka gaida mummyn taka yazeed yahade rai ya kauda kai yana kurban juice tahir yace safana nizan wuce mikewa yazeed yayi idonshi yakai hannun tahir dake rike dana yazeenat yayi gaba yace muje har wajan mota suka rakashi kuma har alokacin bai tsaki hannun yazeenat ba a hankali yazeed yaja tsaki gabaki dayansu suka kalleshi tahir yace yadai girgiza

kai yace nothing wani mugun kallo yawatsa ma yazeenat takauda kanta ta tura mai baki tahir yashiga cikin mota yace to safana sai kunzo gaida su mummy sannan yakalli yazeenat ya daga mata hannu yace bye buddy sai minyi waya dagamai hannu itama tayi tana murmushi har yabar gidan yazeed yakabe hannun tajuyo dasauri tace kai yaya tsaki yaja yace sai koya yagane cewan kina son tahir yayi gaba tabishi dasauri tace ni ni wallahi banface ina sonshi ba
[9:03am, 2/11/2016] presido: 0_09_ bai juya yakalle taba yace kince mana tunda har kina nuna ma duniya kina sonshi yayi cikin parlo dasauri tabi bayanshi tana mai magiya a tare suka samu waje suka zauna mami tace yakuma dawo yanzu bakuma muda kwanciyan hankali a shagwabe yazeenat tace mami wai fa cewa yayi ina son ya tahir dan kawai ina mai bye bye yazeed yace mami duk wanda yakalli yarinyan nan yasan tana son tahir nandanan idon yazeenat yacika da kwalla tace ni wallahi ba sonshi nakeyi ba ko daddy murmushi yayi yace toke dazama kiyi auranki yazeed yahade giran sama da kasa yatashi yabar parlon yazeenat tamike itama tawuce dakinta mami da daddy suka bisu da kallo sannan daddy yace gobe fa yakumbo zata zo dan haka sai kisa agyra mata sashinta mami ta amsa da to
[9:25am, 2/11/2016] presido: 0_010_ washe gari biyu na rana yama yakumbo a kaduna tare da yusuf din baban safana suka taho sashinta kai tsaye aka Wuce da ita dan idan tazo anan take sauka murna agurin yazeenat ba'a magana dan cewa tayi zata tattara kayanta takoma cen wuni ranan yazed bai wuni agida ba yanacen wajan frnds yazeenat kam anacen an makale ma tsohuwa yazeed ne yashugo dakin tare dai sallama bai zauna ba sai da yadauki remote yakunna AC yana hararar yazeenat yace shin kema yakumbo kin zama yar kauyen ce da bazaki kunna AC ba duk uban zafin nan yasamu kujera yazauna zaman mutum daya cikin fararen sol da suka mamaye dakin yazauna yaharde kafa yana karkada yan mukullayren shi dake like jikin wani key holder mai tsinannan kyau ta turo baki gaba yanda take mai inya bata haushi tamike zata fice sai yadan zamo daga cikin kujera yamika dogayen kafafunshi suka tade ta tafadi kif bisa kafet da baka yace good gobe ma ki Kara zumburo mun baki Allah yakumbo yazeenat ta raina ni yakumbo tace waya janyo duk baku kuka soba da mukayi me kun fini sani ai don Allah shashanshun wofi yazeenat tamike tana karkade kayan jikinta tana yatsuna kamar wadda aka tura cikin yumbu yace yakumbo bakya yi mata fadan turan bakin data keyi a hasale kamar ta rufe shi da duka ta dago daga gurzar goron data keyi tace banayi din nace baku kuka so ba sannna tadan sassata muryanta tace sau yaushe kuka shirya kawar da yazeenat ne yazeed yayi wani iri da fuska alamun bai gane hausar ba yace bangane mu kawar da ita ba sai kace wata kaya yakumbo tace to nufina yaushe zaku aurar da ita ga yarinya kafada daya da uwarta amman har yanzu kun taru kuna wani lailayarta kada ma kai yazeed kaji labari yazeenat daga inda take ta ringa daria yazeed yajuyar da kanshi baisan yama ja tsaki ba yayi kicin kicin da fuska yace wai ke yakumbo bakida zance sai aure aure ita wannan kifin rijiyar ma tana fita ne balle wani mummunan yaganta yace yanasonta yazeenat ta harare shi a ranta tace bari in tura ma haushi nima kaima ba kana da budurwa bq tace a ladabce.
[9:49am, 2/11/2016] presido: 0_011_ yazeenat tace wama yacema bani da saurayi ya yazeed-yazeed ya fiddo ido cikin barazana yace eh baby kinsan abunda kike fada kuwa yakara bude baki kaman zai Kara cewa wani abu kafin ya kara tace sake cewa Allah yakumbo ina da wani saurayi a abuja lokacin da mukaje yin wani wasa achan sunanshi kuma doctor faisal yataba zuwa nanma kuma ki tambayi mami takara duban yakumbo da dukkam idanu tana murmushi dake kara mata kyau da kwarjini lokaci daya tana satar kallon yazeed da wutsiyar marassa lafia

idanunta dan ganin irin sukar da kalaman takeyi ba shakka taga sauyawar fuska da idanuwanshi baki daya sun canza kala a hankali tace yakumbo dogone kyakkyawa jajur dashi kaman balarabe hancin sa zirit irin na ya yazeed muryar shi.... Haba yazeed yagama zuwa wuya tun kamin takarasa tuncan fa sauraronta yakeyi absent_mindedly da tunanin ba yazeenat ke wannan maganar ba yarinyan dahar kullin yake gani as a kid baisan yaushe bakinta da idanunta suka bude ba har itace take yabom saurayi a gaban sa baisan sanda ya cafke hannayenta duka biyu ba yana kallon cikin ido da idanuwanshi dasuka rine completely har wani blue blue suka koma suka rine da abinda bata taba gani ba yazeenat ta durkushe gaban yakumbo shima yabita ya durkushe yana huci kaman yumwantaccen zaki yace maimaita abunda kika fadi yanzun yazeenat yakumbo bataji sosai ba ta tsorata ta razana kwarai da yanayin sa haka dakuma irin rikon daya ma yazeenat din yakumbo tace sakar mata hannu sake ta nace idan ka karyata fa da alama bai jin abunda yakumbo ke fadi domin gaba daya baya a hayyacinsa yace in karya ta saime yakumbo yanzu wannan tsakuwar yarinyan ce take yabon kyauwun saurayi inata koyo fitsara yazeenat tace nafada din yakumbo shi ranan yana istanbul dana kirashi wata inyamura ta dauka tace wai... yazeed yakara tsananta matsar dayayi mata ta saki kara dakarfi don zafi amma bakinta bai mutu ba hakannan batayi shuru ba da gayama yakumbo yanda sukayi da yarinyan yazeed yace nace dake nasanta dakarfi yazeenat tace wallahi yakumbo yasanta cewa tayi fa yashiga wanka idan baisan taba yaza ayi har tasan inda yake wanka waya sani ma.. Yazeed yasoma daldalle mata baki da yatsun shi da karfi nandanan dan bakin yahaye daidai lokacin

0_013_yusuf yace wonderful abin mamaki cikin gidan nan Wanda ba Wanda yataba gani wai yazeed da yazeenat yau aka gani a rana su kansu sunji kunya ba kadan ba don haka ba wanda ya amsa mishi kowanne sai huci yake kaman ya cinye dan uwansa yakumbo ta tabe baki ta sunto wani goron a habar zaninta ta kwashe wanda ta gurza a magogi ! Sannan tace aikai kadan kagani bakaji ba har tonon asiri sukewa junansu yazeed yayi tsaki yatashi yafice yusuf yayi murnushi nan yazeenat taringa basu labarin yarinyan yusuf yace to meye abun jin haushi anan aurefa zayyi kema haka sai tamike tana kunkuni na alamun rashin yarda ita kam baza ta tabayin aure ba sabida yayanta shine abokin rayuwarta kuma takuma jin yana mata hirar wata budurwanshi dole suci gaba da fada

Edited · Like · 4 · Reply · Edit · 6 minutes ago

Rukayya Muhamad Aboki Ruky

0_014_ saida yakumbo tayi kwana biyar sannan a kwana na shida ne suka shirya komawa safana ita da yusuf daddy yace yazeenat da yazeed su bisu ransu yamatukar baci dan fushi sukeyi da juna a motar hajia yakumbo akayi tafiyar daga yazeed har yazeenat ko wannan su shan kamshi yakeyi har suka kai zaria babu wanda yakuma magana hannu yakai yakunna wakar sani aliyu ta shehu kangiwa jagowaran sokoto yana kada kai cikin nishadi yana rangaji da dogon wuyanshi yana buga sitiyarin da hannunshi daya dayan ko yana cigaba da tukinsa hankali kwance yana bin wakar da rythm din da mawakin yayi amfani sak! Yazeenat ta kama kanta da hannu bibbbiyu tuni kanta yasoma sarawa ta tsani melody na wannan wakar domin ciwon kai yake haifar mata tun ba yauba tasha gayawa ya yazeed duk cikin kasunsunan shi ba wanda ta tsana irin wannan kaset din tun kuma daga ranar bai Kara sawa ba to yau ko don yana jin haushin tane oho sai ta kwantar da kanta cikin cinyoyinta tayi shuru kanta na cigaba da sarawa sunyi nisa sosai ya gyara murya ya kure sautin sosai yanda su yakumbo baza suji

abunda yake fada ba yazeed yace wayyo ronke nayi missing dinki amma by the way nakusa zuwa inda kike da yanzu muna makale da juna a hankali yazeenat tayi tsaki baya ga wani tukuki daya zo ya tokare mata a kahon Zuciyanta lallai ma yayanta din da bata hada kowa dashi ba yau a gabanta yake cewa yayi missing wata kwalla suka cika Mata ido ta dago ta dube shi tace ai saika aje mu ka koma can wajan rakiyar tunda kuwa kuna wanka tare ba dole kayi kewar taba yazeed yayi daria sosai sabida rakiyar datace yabashi daria sosai yace ke sis wanka da ronke shine yadame ki niko kyakkyawan fuskarta nake kewa dan kuwa shigarta tana burgeni takuwa shaka ta kule tahaye suntum fiye da tsammanin sa ko nunfashi da kyar take yi wai a gabanta ya yazeed ke wannan kazamar maganar amma Allah wadaran wannan ronke din data gurbata mata tarbiyan yayanta shiko yazeed ko ajikinshi har wani lumlum yake da ido wai yana tunanin ronke!

[9:30am, 2/18/2016] presido: 0_15_ kwana daya sukayi yazeed yana mota ya daura kafansa jikin kujera bayan mota tashiga takame yakai hannu ya shafi kyakkyawan saisayen kanshi zuwa dokin wuyanshi ya dubeta idanuwanshi sunyi kasa sosai Kaman suna neman rufewa don kansu yace nayi maki kama da ado direba ne Allah ko ronke danake mutuwar so bata isa ta kame a owner side ba in tukata Allah wallahi kuwa baki isa ba don haka cikin biyu dole ki zabi daya kodai ki komq gidan tsohuwar da kika fito ko kuma ki komo mazaunin mai zaman kansa don kowa yaganki yasan zaman banza kike sai ya gyada kai kamar kadangaruwa zuciyar nan basai an tona ba don takaici tafito ta banka kofa tafada cikin gida taja kujera tazauna tana cika tana batsewa kiris take jira tafashe yakumbo tace ke lafia me kuke jira tun dazu baku tafi ba anya yayyan nan kuna jiyewa kanku tafiyar dare kuwa yazeenat tace aa yakumbo ba laifina bane yq yazeed ne yace in dawo a bani kudin mota in je ata haya yakumbo tace akan wane dalili kiga mun dan nema bari inje in tadda shi taja gyalenta tayi waje kafar sa daya cikin motar daya a waje yana bin wakar Hassan sarkin dogarai ta dacta mamman shata don shi yazeed akwai shi dason wadannan wakokin namu na gargajia sune hobby dinshi
[9:52am, 2/18/2016] presido: 0_16_ yakumbo ta tsaya akanshi Na yan dakiku batare Daya sani ba ta nazarci abubuwa masu dama a tare dashi Cikin Yan dakiku sannan tace wane irin neman magana ne wannan yazeed wai meyasa kuke haka ne kai da yar uwarka kuma ai sai kowa yayi muku daria ya rage sautin radiyon yace saiki tambayeta dalilin ta na kamewa a baya in tukata ance da ita ni direban gidan sune yakumbo tayi daria irin tasu ta manya amma zuciyar ta tayi nauyi har yaushe zasu dauwama suna boyewa mutane wannan sirrin yanzun ta fahimci yana neman zama cutuwa ko kwara ga yazeed da ita kanta yazeenat har yaushe za'a dauwama a hakan ko makaho yashafa idanun su zai bada tabbacin soyayya suke su kansu basu saniba ita kam tana ganin dq yakubu yayi tunani dabai dauki matakin boye wannan alamari ga kowa ba tunda ko wata rana yazeenat zatayi aure zancen duniya baya taba boyuwa koda kuwa a karkashin gado aka sanyashi karan motar ne yamaido da ita daga duniyar tunani ta dubi yazeenat tace aa shugo gaban ku tafi sannna tadubi yazeed tayi murmushi tace da abokan wasa kuke sai ince son junanku kuke amma duk wannan ce ce kuce banga dalilin saba sai aka ce wani Abu zai ragu a jikin ka don yazeenat ta zauna a bayan Mota ka tukata yayi saurin cewa Allah yaso basu din bane kosu dinne Allah yakumbo banga abunda zanci da wannnan kodaddiyar yarinyan ba yazeenat takai hannu a hankali tashafo dogon hanncin ta takare masa kallo tsaf cikin yan dakiku taso ace akwai makusa a tattare da yazeed dayau ta rama wannan

cin fuskar amma babu komai nasa yayi masa daidai yakuma dace da yadda ubangijin halitta ta tsara mishi abinshi kai kace shi ya zabawa kansa tako ina ya yazeed baida makusa ita ko tasan farace jazur kenan farin ta yayi yawa har ta kode wasu kwalla suka zubo mata shar tayi saurin sharewa da bayan hannunta yakumbo ta rasa ma Abinda zatace tace oh ni Allah kayi mun maganin abinda yafi karfina ka iya min abinda bazan iya ba
[10:12am, 2/18/2016] presido: 0_17_ tafe suke tamkar kurame to ba Wanda yace da dan uwansa ci kanka har suka fita a katsina kwata kwata yazeed a ransa yace bari dai yakara tsokanota ya dibi yanayin ta sannan yamaida hankalinshi kan titi yace kinsan meye cweet sis Abinda ke kara sawa inso ronke shine murmushin ta tamkar yammatan hurul_eeni tafiyar tako kinsan catwalk to haka take idan tayi daria jerarrun hakoranta masu haske kamar kankara na sawa in mance da kowacce ya mace a duniya muryar ta tamkar ana busa sarewa tana kishina kamar mijinta ranar da kika yo mun waya kwana tayi tana kuka idan ta rumgume ni yazeenat mancewa nake da kyawun kowacce diya mace a duniya sai ita ronke adeyemi olayimi sai a lokacin ya lura yazeenat kuka take haikan kuka take tun karfinta baka da zuci nandanan zuciyar sa ta tsinke hade da wani mummunan faduwar gaba duk wani haushinta dayake ji sai yakau komi ya tsaya mai cak sai ya tsinci kansa dajin tausayin kansu balantana ma ita yazeenat shifa ba mahauci bane hakannan a shekarun sa da tunanin sa da matakin iliminsa ya isa ya fahimci irin kaunar da suke wa juna daban take da wadda yan uwan jini daya ke yiwa junan su kar dai ya kasance Allah ya jarrabcesu da son juna A'uzu billahi Minash - shaitanir-rajeem waje yasamj yayi parking cikin karfin hali yace yazeenat haba lil buddy na hadaki da girman Allah kiyi hakuri ni wasa nake Allah amma da alama naga kin maida abun da gaske daga yazeenat no response ba amsa kai kace da zaunnan nan dutse yake magana yayi shuru yama rasa ta inda zai fara ya langabar dakai jikin seat dinShi abin tausayi don dai ta tabbatar yayi nadamar cikin tattausar muryar shi yace
[10:22am, 2/18/2016] presido: 0_18_ yanzu ke sis in akace dake ina aikata Abinda nake fadi saiki yadda nayi zaton kinfi kowa sanin halina a hankali tace toni ya yazeed ina ruwana kome kaji nace kai kadai fa kake maganar ka kake kidan ka kake rawarka ba matse ma baki nayi ba inma kayi din meye ba mami tace lokacin kane ba yayi murmushi a ransa ko cewa yake yaushe yazeenatzata girma ne komi nata akwai kuruciya aciki at 28 a kalla yabata shekara 6 don haka lallashin ta bazai yi wuya ba yace alright na amsa wannnan nidai so nake kiyi hakuri nasan ranki yabaci gashi mun kusa zuwa gida bana son mamin mu taganki a haka very upset don zata tambayeni ko gashi kuma bansan mezance mataba ta turo baki sabida matukar haushin daya bata ta soma motsi da jikinta a hankali cikin tadin zuci batasan har maganar ta yafito fili ba a wane dalili raina zai baci sabida yayana ta
[10:40am, 2/18/2016] presido: 0_19_yayana yayi budurwa this is sheer nonsense shirme banza ne kawai ta girgiza kai sai kuma hawaye suka zubo ya lakato hawayen yana murmushi yace yhu see ranki yabaci hawaye sunkan zubo a dalilai guda biyune kawai bacin rai ko tsananin farin ciki yazeenat daki zubar da hawayenki a domina gara kisa dorina kiyi ta dukana harsar na suma your tears mean alot to me amma bazaki gane hakan ba a yanzun share hawayen nan maza maza don Allah badon niba muryar ta na rawa kasa kasa cikin rishin tace naji yayi murmushi yace ba haka nake son amsar ba cewa zakiyi ya yazeed dina komi yawuce na hakura sa'annan regain ur mood yazeenat dina tashafi goshinta zuwa siraran labbanta da yan yatsun ta na dama itadai har yanzu ronke na ranta ta daure tace shin wacece ronke yazeed

